Asiwaki mai tsarkake baki ne, mai sa yardar Ubangiji ne

Daga Aisha - Allah Ya yarda da ita - ta ce: Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - yace: "Asiwaki mai tsarkake baki ne, mai sa yardar Ubangiji ne".
[Ingantacce ne] [Nasa'i ne ya ruwaito shi da Ahmad]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - yana sanar damu cewa tsaftace hakora da itaciyar urak da makamancinta yana tsaftace baki daga datti da wari wadanda suke abin ki. Kuma cewa shi yana daga sabubban yardar Allah ga bawa; domin cewa a cikinsa akwai biyayya ga Allah da amsa umarninSa, da kuma abinda ke cikinsa na tsaftar da Allah - Madaukakin sarki - yake son ta.

http://www.sunnah.global/hadeeth/ha/show/3588